Lallai cewa Manzon Allah SAW Mala'ika Jibril ya zo masa kuma shi a halin yana wasa da Yara, sai ya kama shi ya sumar da shi, kuma ya tsaga Qirjinsa, ya futo da Zuciyarsa, sai ya futar da wata tsoka daga cikinta, sai ya ce: wannan shi ne rabon Shaixan daga cikinka"

Daga Anas Bn Malik -Allah ya yarda da shi- Lallai cewa Manzon Allah SAW Mala'ika Jibril ya zo masa kuma shi a halin yana wasa da Yara, sai ya kama shi ya sumar da shi, kuma ya tsaga Qirjinsa, ya futo da Zuciyarsa, sai ya futar da wata tsoka daga cikinta, sai ya ce: wannan shi ne rabon Shaixan daga cikinka, sanna ya wanketa a cikin wata Tasa ta zinare da ruwan zam zam, sannan ya mayar da ita ya inda take, sai Yara suka zo suka gayawa Mahaifirsa -Mai Shayar da shi- suka ce: lallai Muhammad an kashe shi, sai suka gamu da shi launinsa ya canza Anas ya ce: "Kuma ni na kasance ina ganin wurin xinkin a qirjinsa"

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/10862